

A ranar Lahadi ne dai, iyayen Manu suka sayo mishi jan rigan ruwa.
Sai Manu ya tambayi babarshi, "Umma, zan iya sawa yanzu?"
Sai ta ce, "A'a, abin so na, an dai kusa fara ruwan sama, amma yanzu sararin sama yana nan dahaske."



Litinin ta kasance da hasken rana.
Sai Manu ya tambayi Umma, "Za ayi ruwan sama yau?"
"A'a Manu, ba dai yau ba. Idan fa ka sanya rigan ruwa, za ka zam abin dariya!" Umma ta ce.



A ranar Talata ma, sama ta kasance shudiya.

Sai Manu ya ce, "Umma, yaushe burina zai cika?"

Umma ta ce, "Ba yau ba, abin so na, kaga yau ma akwai haske a sararin sama!"



Ranar Laraba ma takasance cikin yanayin zafi.

Sai Manu yayi tambayi Umma, "me ya sa har yanzu ba a yi ruwan sama ba?"

"Ina tsammanin za a yi ruwan sama ba da dadewa ba.

Watakila ma kafin da rana," Umma ta ce.



A ranar Alhamis Manu zai tafi yawon shakatawa.

Sai Manu ya ce, "Umma da yiwuwa a yi ruwan sama, Shin in dauki rigan ruwa tare da ni?"

Sai Umma tace, "A'a, ba za ayi ruwan sama ba yau. Kaga ai sararin sama da haske,"



Ranar Jumma'a ta kasance da hadari.

"Umma, za a yi ruwan sama yau?" In ji Manu.

Sai Umma ta ce "Da alaman haka, Tunda akwai hadari a sararin sama,"



Ranar Asabar ta fara da tsawa!

Ji kake Badaboom!

"Umma, shin wannan tsawa nake ji? Za a yi ruwan sama ba dadewa ke nan?" Manu ya tambaya.



Daga ƙarshe dai, sai gashi an fara ruwan sama!

"Yeeeii, an fara ruwan sama, an fara ruwan sama."

Manu, yafito da gudu yana murna.